# Wakili na MENA



Mun yi la'akari da matsayinka a matsayin wani wanda ya zo daga Gabas ta Tsakiya da kuma Afirka ta Arewa (MENA a taƙaice), wato wani ƙaramin yaro baƙo wanda ya zo daga ƙasar waje da ba ya tare da kowa.

## Mene ne ma'anar «MENA»?

Tana nufin cewa:

- Kana ƙarƙashin shekaru **18** na haihuwa
- Ba ka da zama ɗan ƙasa na Ƙasar Belgium
- Iyayenka ba sa tare da kai a cikin Belgium
- Ba ka da wani izini mai inganci na zama a cikin

A cikin Belgium, ƙananan yara baƙi daga ƙasar waje waɗanda ba sa tare da kowa suna da haƙƙi na samun wani **wakili.**

FEDERAL PUBLIC SERVICE
JUSTICE



## Amma... mene ne wani wakili ke yi?

Wakili wani mutum ne wanda muka zaɓa don ya ba ka tallafi da taimako a gare ka a cikin rayuwarka ta yau da kullum a cikin Belgium.

Ita ce wakiliyarka/Shi ne wakilinka ta fuskar shari'a: wannan yana nufin cewa za ta riƙa ko zai riƙa taimaka maka da duka hanyoyi da ya kamata ka bi don zama a cikin Belgium. Ga misali, idan kana neman mafaka ko neman zama a cikin Belgium, za ta kasance tana nan/zai kasance yana nan don ba ka tallafi da taimako gaba ɗaya a kan hanyar da ta dace da za a bi.

Wakili yana yin wasu abubuwa, fiye da haka. A nan ga wasu misalai kaɗan:

- Takan/Yakan ziyarce ka a-kai-a-kai
- Takan/Yakan yi maka bayanin abubuwa da hukumomi suka zartar game da kai



- Takan/Yakan nema maka wani lauya da zai yi maka aiki kyauta domin kai
- Takan/Yakan binciki cewa kana jin daɗi a cikin masaukinka kuma, idan ya zama dole, a taimaka maka samun masauki da ya dace
- Takan/Yakan yi maka rijista da makaranta da kuma tabbatar da cewa kowane abu yana tafiya daidai a makaranta
- Idan kana da wasu matsalolin kiwon lafiya, za ta/zai tabbata ka sami duka kulawa da kake buƙata
- Takan/Yakan sarrafa kuɗinka a cikin shawara tare da kai
- Lokacin da abubuwa ba sa tafiya daidai, takan/yakan saurari matsalolinka
- Takan/Yakan girmama ra'ayinka da abubuwa da ka yi imani da su
- Takan/Yakan yi magana da kai game da makomarka
- Idan kana so, za ta/zai taimaka maka ka nemi iyayenka

Idan kana da wasu tambayoyi game da ayyukan wakilin naka, za ka iya magana da ita/shi.

## Har yaushe za ka sami wani wakili?

Wakilin naka zai tallafa maka har sai ka kai shekaru 18 na haihuwa. Lokacin da ka kai shekaru 18, ka zama mai cin gashin kanka.

**Mene ne wannan ke nufi?**

Yana nufin cewa ya zama wajibi ka kula da kanka. Wakilin ba zai sami damar ci gaba da yanke shawarwari domin ka ba. Amma kada ka damu, wakilin naka zai taimaka maka shirya bikin ranar haihuwarka ta shekaru 18: za ta/zai ba ka shawara da samar maka da bayani na abin da ya kamata ka sani.

Duk da haka, zai iya yiwuwa aikin wakilin naka ya ƙila tsaya kafin ka kai shekaru 18: idan iyayenka suka iso cikin Belgium, ko idan ka bar Belgium. A irin waɗannan lamura, za mu aika maka wata wasiƙa da za ta ce yanzu ba ka da sauran wani wakili mai kulawa. Wakilin zai tattauna wannan tare da kai.

## Mene ne yakan faru idan kana da wata matsala tare da wakilin naka?

Dole wakilin ya saurare ka da kuma zama wanda za ka iya samu a lokacin da kake buƙata. Gwada yi mata/masa magana game da abin da ba daidai ba.

**Mene ne zai faru idan hakan ba ya aiki?**

- **Sami haɗuwa tare da mu;** za mu iya gwada warware maka matsalar.
- Za ka iya kuma zuwa ga Alƙalin Lumana. Ita ce wadda ke nan da za ta/Shi ne wanda ke nan da zai warware maka matsaloli tsakaninka da wakilin naka. Za ka iya tambayar mu don ƙarin bayani ko ka tambayi ma'aikacin zamantakewa a cibiyar karɓar baƙi ɗinka.



## Ta yaya za a tuntuɓe mu?

Za ka iya tuntuɓar mu sa'o'i 24 a cikin mako (24/7) a kan wannan lambar tarho:

078/15.43.24

Za ka iya kuma aika imel zuwa ga:

tutelles@just.fgov.be

Idan kana da buƙatar taimako tuntuɓe mu, za ka iya tambayar ma'aikacin zamantakewarka a cibiyar karɓar baƙi ɗinka ko lauyanka.

RESPONSIBLE EDITOR: JEAN - PAUL JANSSENS BD DE WATERLOO 115 -1000 BRUSSELS D/2021/7951/EN/1237